## SŨRATUL GHÃSHIYA سُورَةُ الغَاشِيَةِ

Tana karantar da yin hujja da abin da ake iya gani da ido dõmin a fahimci abin da ake gani da hankali, gwargwadon tunanin abokin magana.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

هَلْ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ٱلْغَٰشِيَةِ ١

*1.* Lalle ne labãrin (Kiyãma) mai rufe mutãne da tsõronta yã zo maka?

وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ خَٰشِعَةٌ ٢

*2.* Wasu huskõki a rãnar nan ƙasƙantattu ne.

عَامِلَةٌ نَّاصِبَةٌ ٣

*3.* Mãsu aikin wahala ne, mãsu gajiya,

تَصْلَىٰ نَارًا حَامِيَةً ٤

*4.* Zã su shiga wata wuta mai zãfi.

تُسْقَىٰ مِنْ عَيْنٍ ءَانِيَةٍ ٥

*5.* Ana shãyar da su daga wani marmaro mai zãfin ruwa,

لَّيْسَ لَهُمْ طَعَامٌ إِلَّا مِن ضَرِيعٍ ٦

*6.* Ba su da wani abinci fãce dai daga ɗanyi.

لَّا يُسْمِنُ وَلَا يُغْنِى مِن جُوعٍ ٧

*7.* Bã ya sanya ƙiba, kuma bã zai wadãtar daga yunwa ba.

وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ نَّاعِمَةٌ ٨

*8.* Wasu huskõki a rãnar nan mãsu ni'ima ne.

لِّسَعْيِهَا رَاضِيَةٌ ٩

*9.* Game da aikinsu, masu yarda ne,

فِى جَنَّةٍ عَالِيَةٍ ١٠

*10.* (Suna) a cikin Aljanna maɗaukakiya.

لَّا تَسْمَعُ فِيهَا لَٰغِيَةً ١١

*11.* Bã zã su ji yãsassar magana ba, a cikinta.

*12.* A cikinta akwai marmaro mai gudãna.

فِيهَا عَيْنٌ جَارِيَةٌ ١٢

*13.* A cikinta akwai gadãje maɗaukaka.

فِيهَا سُرُرٌ مَّرْفُوعَةٌ ١٣

*14.* Da kõfuna ar'aje.

وَأَكْوَابٌ مَّوْضُوعَةٌ ١٤

*15.* Da filõli[1] jẽre,

وَنَمَارِقُ مَصْفُوفَةٌ ١٥

*16.* Da katifu shimfiɗe.

وَزَرَابِيُّ مَبْثُوثَةٌ ١٦

*17.* Ashe, to, bã zã su dũbãwa ba ga rãƙumã yadda aka halitta su?

أَفَلَا يَنظُرُونَ إِلَى الْإِبِلِ كَيْفَ خُلِقَتْ ١٧

*18.* Da zuwa ga sama yadda aka ɗaukaka ta?

وَإِلَى السَّمَاءِ كَيْفَ رُفِعَتْ ١٨

*19.* Da zuwa ga duwãtsu yadda aka kafa su?

وَإِلَى الْجِبَالِ كَيْفَ نُصِبَتْ ١٩

*20.* Da zuwa ga ƙasa yadda aka shimfiɗã ta?

وَإِلَى الْأَرْضِ كَيْفَ سُطِحَتْ ٢٠

*21.* Sabõda haka, ka yi wa'azi, kai mai yin wa'azi ne kawai.

فَذَكِّرْ إِنَّمَا أَنتَ مُذَكِّرٌ ٢١

*22.* Ba ka zama mai ĩkon tanƙwasãwa a kansu ba.

لَّسْتَ عَلَيْهِم بِمُصَيْطِرٍ ٢٢

*23.* Fãce dai duk wanda ya jũya bãya, kuma ya kãfirta,

إِلَّا مَن تَوَلَّىٰ وَكَفَرَ ٢٣

*24.* To, Allah zai yi masa azãba, azãbar nan da take mafĩ girma.

فَيُعَذِّبُهُ اللَّهُ الْعَذَابَ الْأَكْبَرَ ٢٤

*25.* Lalle ne, zuwa gare Mu kõmõwarsu take,

إِنَّ إِلَيْنَا إِيَابَهُمْ ٢٥

*26.* Sa'an nan lalle ne aikinMu ne Mu yi musu hisãbi.

ثُمَّ إِنَّ عَلَيْنَا حِسَابَهُم ٢٦

(1) Matãsan kai.